# Littafi mai Tsarki na yara

## Ke gabatar da

# Ezekiyel: Mutum mai Ru'uyoyi



**Wanda ya Rubuta: Edward Hughes**

**Mai Zane: Lazarus**
**Alastair Paterson**

**Mai niyyan daukan nauyi: Ruth Klassen**

**Fassarawa: Bible Society Nigeria**

**Wanda ya Wallafa: Bible for Children**
**www.M1914.org**

**©2024 Bible for Children, Inc.**
**Zaku iya kofan wanna labarin ku wallafa idan**
**har ba zaku sayar da shi.**

**Tun da daddewa, sojoji masu karfi sun kai wa Yahuda hari, suka kwashe mutanen Allah zuwa zaman bauta a kasar Babila. Da nesa daga gida, Yahudawan an sun zauna a gefen kogin Kebar. A cikinsu akwai bawan Allah, annabi Ezekiyel.**



Wata rana, Allah ya ba wa Ezekiyel wahayi. Daukakar Allah ta bayyana kamar haske mai karfi, a siffar halittu hudu masu ban tsoro. Kowanensu yana da fuskoki hudu da fikafikai hudu.  A kansu akwai kursiyi na safaya mai kyakyauwa, cike da haske mai kunna da kalar gajimale.  Sa’ad da Ezekiyel ya gan shi, sai ya fadi da fuskarsa
har kasa.



Allah ya yi wa Ezekiyel magana.  “Ina aike ka ga ‘ya’yan Isra’ila.  Yi magana Kalmomina garesu, gama su ‘yan tawaye ne.”  Sai hannu ya bayyana, rike da naddaden littafi.  “Ka ci wannan littafin,” Allah ya ce, “sai ka tafi, yi magana da gidan Israila.”  Ina umurnin da bai yi daidai ba!



Amma Ezekkiyel ya yi biyayya, ya cinye littafin ya tafi.

**Ruhun Allah ya daga Ezekiyel ya dauke shi zuwa inda Yahudawan da suke bauta a wani wuri a Kogin Kebar. Ya yi kwana bakwai yana zama inda suke zama, yana mamakin abin da yake gani. Sai Allah ya mai da Ezekiyel mai gadinsu. Zai ja musu kunne don kada su yi rashin biyayya ga Allah.**





**Ezekiyel ya yi abubuwa dabam-dabam don ya sa kalmar Allah ta sami fahimta daga mutanen. Ya yi zanen hoto na Urushalima a fefen laka. Watakila akwai wadansu da suke leka a bayansa yayinda yake zane wani babban kungiyar sojoji kewaye da Urushalima. Yana nuna cewa birni mai tsarki na Allah ba da daddewa ba, za a halakar da shi.**

Isra’ila, mulki na arewa, sun yi wa Allah rashin biyayya na shekaru dari uku da casa’in (390), sa’an nan Yahuda mulki na kudanci, sun yi rashin biyayya na shekaru arba’in (40). Shi ya sa an halakar da Isra’ila, kuma Yahuda zai halaka ba da daddewa ba. Allah ya gaya Ezekiyel ya kwanta a gefen hagunsa na kwanaki 390, sa’an na ya kwanta a hannun dama da kwanaki 40, don ya tunashe mutanen yawan shekarun zunubansu.





**Watakila mutanen sun fara tunani cewa Ezekiyel mutum ne wanda ba za a iya fahimta ba. Ya yi duka abin da Allah ya gaya masa ya yi. Wata rana, ya yi askin summan kansa sai ya kone sashi na uku. Wannan ya nuna cewa sashi na uku na mutanen Urushalima za su mutu don cuta da yunwa sa’ad da sojojin Babila suka kai wa birnin hari.**





**Ezekiyel ya dauki wani sashi na uku na summan sa ya yayyanka shi da takobi. Wannan don ya nuna cewa wani sashi na uku za su mutu daga takobin sojojin abokan gaba. Sashi na uku na karshen, Ezekiyel ya watsar da shi a iska. Amma ya dinka wadansu 'yan summan a gindin rigarsa, alama cewa Allah zai ajiye wadansu mutanensa**



**lafiya lau sai ya komar da su zuwa Kasar Alkawari.**

Wannan annabi mai karfin hali ya gaya wa Yahudawan da suke kasar bauta cewa abubuwa za su kara dagullewa, ba kamar yadda suke zato za su gyaru ba. Mutanen suka yi fushi da Ezekiyel, amma ya ci gaba da yin magana a kan Kalmar Allah. Wata rana, sa’ad da yana zama da dattawan Isra’ila, Allah ya ba wa Ezekiyel wahayi. A cikin wahayin, Allah ya daga shi sama ta summan kansa ya kai shi haikali a Urushalima.



**A cikin Haikalin, Allah ya nuna wa Ezekiyel abubuwa masu tafiya a kasa, dabbobi marar tsabta, da gumaka. Bai kamata wadannan abubuwa su kasance a Haikalin Allah ba.**



**Shugabannin suna sujada ga wadannan abubuwa maimakon Allah. Allah ya kuma nunawa Ezekiyel cewa Daukakarsa yana barin Haikalin kuma za a hallakar da shi. Bayan da wahayin ya kare, Ezekiyel ya gaya wa Yahudawan game da shi.**





**Duka abubuwan da Allah ya fada sun zama gaskiya. An halakar da Urushalima. Mutane da dama suka halaka. Sa'ad da Yahudawan da suke zaman bauta a Babila suka ji wannan, sun fara mamaki ko Allah ya bashe mutanensa har abada.**

**Amma Allah ya ba da wani sako wa Annabinsa.  Ya kai Ezekiyel ga wani kwari mai cike da busheshen kasusuwa – kasuwan mutane.**



“Dan Mutum, kasusuwan nan za su iya sake rayu?” Allah ya tambaye Ezekiyel. “Ya UBANGIJI Allah, Ka sani,” Ezekiyel ya amsa. Tabas babu yadda busheshen kasusuwa za su sake rayu. UBANGIJI ya ce, “Ka yi wa wadanan kasusuwan annabci, ka ce ‘Ya busheshen kasusuwa, kunji kalmar UBANGIJI! Za ku rayu.’” Sa’ad da ya yi biyayya, Ezekiyel ya ji babbar sururtu.
A ganinka me ya jawo wannan?



Yayinda annabin yana kallo cikin mamaki,
jikuna suka fara tattaru kashi da kashi.



Sa’an nan, naman jiki ya sauka a kansu.



Fatan jiki ya rufe su duka, amma babu numfashi a kansu.



**UBANGIJI ya ce, “Yi annabci, dan mutum ka ce ‘Zo daga iskokin numfashi guda hudu. Saka numfashi a kan wadannan don su rayu.’” Bayan da Ezekiyel ya yi haka, numfashi ya sauko a cikinsu. Suka rayu, suka tashi tsaye. Sai babba rundunar sojoji sun cika kwarin.**



**Allah ya sani Yahudawan da suke a Babila sun fid da rai sa’ad da suka ji labarin faduwan Urushalima. Sai ya aiko da sako ta wurin wahayin Ezekiyel. “Wadannan kasusuwa su ne duka gidan Isra’ila,” Allah ya ce. “Zan sa Ruhuna a cikinku, in komar da ku zuwa kasarku.”**



**Babbar sako na bege daga Allah! Alkawarin Allah ta wurin Ezekiyel ya zama gaskiya sa'ad da Yahudawa suka koma zuwa kasarsu. Sun sani UBANGIJI Allah ya dawo da su gida. Kalmar Allah kullum takan zama gaskiya.**



# Ezekiyel: Mutum mai Ru'uyoyi

**Tahiri da ga maganar Allah, littafi mai Tsarki**

**a na samu a**

**Ezekiyel**

**"Shigowar maganar ka yana baduar kawo haske." Zabura 119:130**

# KARSHE

29

60

**Wanan tahiri daga littafi mai-tsarki na mana bayanin Allah mu wanda ya halicce mu wanda yake son mu san shi.**

**Allah ya san da cewa mun yi abubuwan da ba su da kyau, wanda yake kira zunubi. Sakamakon zunubi mutuwa ne, amma Allah ya na kaunan mu sosai. Ya aiko da Ɗansa Yesu, ya mutu a kan giciye ya sha wahala domin zunuban mu. Kuma sai Yesu ya tashi daga matattu ya koma gida a sama. Idan ka bada gaskiya ga Yesu. Ka roƙeshi gafaran zunuban ka, zai yafe. Kuma zai zo ya zauna a cikin zuciyan ka kaima kuma zaka zauna a zuciyar shi har abada.**

**Idan ka yadda da wannan gaskiya ne, Ka cewa Allah:**
**Ya Yesu, na bada gaskiya kai Allah ne, ka kuma zamu mutum don ka mutu domin zunubi na, kuma yanzu ka tashi. Ina roƙon ka, ka shiga cikin zuciya na kuma ka yafe min zunubai na, Domin in samu sabon rai yanzu, kuma wata rana in zauna tare da kai har abada. Ka taimake ni in yi maka biyayya kuma in yi rayuwan da zai gamshe ka a matsayin ɗan ka. Amin.**

**Ka karanta littafi mai-tsarki kuma ka yi magana da Allah a kulla yaumin. Yahaya 3:16**